
***HAUSA – "Peace"***

# SALAMA



"Da ma a ce yanzu kun san abubuwan da ke kawo salama!" Luka 19:42.

Idan muka duba kewaye da mu, muka ga abubuwan da ke faruwa a duniya, za mu gane lalle ba bu salama a duniya. Ko ina za ka ji ana fada yaki da kisa, yake yake da labarum yaki. Ko wane irin jarida ne ka saya, za ka ga munanan labaru a kan abin da mutane ke aikatawa domin zunubi da kiyaya da kishi. Manyan mutane da shugabanni na duniya suna ta kokari shekara da shekaru domin su kawo salama a duniya amma abin ya gaggara. Ba duniya kadai ba amma har da gidajenmu. Mafi muni duka shi ne mutane da yawa a duniya ba su da salama a rayukansu to, a nan ne fa inda damuwan yake.

**ME YA SA BABU SALAMA?**
A cikin farko Allah ya hallici duniya da ciyaye da furane da itatuwa da dukan dabobi da ke rayuwa a kasa da cikin ruwa. Allah ya hallici Adamu da Hawwau. A cikin dukan halitarsa akwai salama. Adamu da Hawwau suna rayuwa tare da dukan dabbobi ban da tsoro. Tinkiya ko rago zai yi kiwo kusa da zaki kumazakin ba zai yi mata kome ba. Bugu da kari akwai salama tsakanin mutane da Allah, kuma Allah yakan zo sanyin yamma ya yi hira da Adamu da Hawwau. Ba su tsoron Allah a zukatansu, kuma suna marmarin ya zo ya ziyarce su. Sai Shaidan makiyin salama ya shiga maciji ya zo ya jarabci Adamu da Hawwau don su yi zunubi, domin ya san cewa inda akwai zunubi to fa, ba zaman lafiya ko salama.

Shaidan shi ne uban kararayi, ya fada musu cewa idan sun yi rashin biyayya ga Allah ba lalle zasu mutu ba idan suka ci daga itacen. Kamar yadda ko a yanzu ma mutane sun fi kasa kunne ga muryar Shaidan, ta haka Adamu da Hawwau sun yi abin da Shaidan ya jarabce su su yi, sai nan da nan salama da suke da shi ta rabu da su- dukan salama da abubuwa masu kyau da Allah ya halitta dominsu duk sun lallace cikin wannan abu daya da suka yi, sai tsoro ya shiga cikin zukatansu.

Da yamma Allah ya zo a daidai lokacin da ya saba zuwa, sai Adamu da Hawwau suka boye domin suna jin tsoro kasancewar Allah. *"Zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutum daya, zunubi kuwa shi ya kawo mutuwa"* Ko mu da muke raye a yanzu, mun yi zunubi kuma mun yi nesa da Allah (Romawa 5:12; 3:23). Zunubi daya yakan kai ga wani shi yasa duniya duka ta kamu da da zunubi, shi ya sa babu salama a duniya.

**ALLAH YA SO YA SAKE MAIDO DA SALAMA A DUNIYA**
Allah daga sama ya duba duniya sai ya ga kiyaya da tsoro da zunubi da bakin ciki, sai a cikin kaunarsa mai girma ya aiko da dansa domin a haife shi a cikin tsakarkani. A kowane shekara a ranar Krismati ana tuna mana da sakon malaika, "Kada ki ji tsoro, ga shi albishir ina kawo maku farin ciki mai yawa wanda ya zama na dukan mutane ne. Ba labari sai ga taron rundunar sama tare da mala'ikan nan, suna yabon Allah suna cewa "Daukaka ga Allah ta tabbata, can cikin Sama mafi daukaka. A duniya salama ta tabbata ga mutanen da yake murna da su matuka." (Luka 2:10-14). Yesu Kristi an turo shi duniya ne "Domin ya hashaka na zaune cikin duhu da wadanda suke zaune a bakin mutuwa." (Luka 1:79). Afisawa 2:14 ya fada mana cewa "Domin Almasihu shi ne salamarmu, shi wanda ya mai da Yahudawa da al'umai daya." Allah ya turo mana Sarkin Salama, da mutane za su karbi wannan Sarkin salama, da mun yi zaman jituwa a duniya.

**ME MUTANE SUKA YI DA WANNAN SALAMAR?**
Kamar Adamu da Hawau, Yahudawa da sauran mutane a lokacin, sun

zaba su yi wa Allah rashin biyayya, su kuma bi shawarar Shaidan. Sun ki Sarkin Salama, kuma lokacin da Bilatus ya basu damar zaben wanda za a sake tsakanin Yesu da Barabas, sai suka yi ihu suka ce “A gama da Yesu, a sake mana Barabas.” Wato suna cewa “a kawar da mai kawo salama, sai a ba mu kiyayya da yake yake, da kisankai da zunubi.” Wadannan mutane suna da ikon yin zabe da kansu ba tare da tilastawa ba, amma sai suka zabe Barabas. A cikin kwanakin na yanzu ma abin haka yake. Allah ya ba mu zabe. Za mu iya zabi Yesu a rayukanmu ya zama mai cetonmu da Sarkinmu, zai kuwa kawo salama a rayukanmu. Yace, “Na barku da salama, salamata nake ba ku. Ba kamar yadda duniya ke bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada kuma ku ji tsoro.” (Yahaya 14:27). Zunubai da suke a rayukanmu sun kawar da mu nesa da Allah. A halin da muke ciki na zunubi, ba zai yiwu mu sami salama a bisa kanmu ba. Amma Yesu yana nan kullum da hannu bude domin yana shirye don ya maido da mu, ya zama da mu ‘yayan Allah, yaba mu **SALAMA.** An fada mana a Romawa 5:1 cewa “To, da yake mu kubutattu ne ta wurin bangaskiya, muna da salama ke nan a gun Allah, ta wurin Ubangijinmu Yes Almasihu! Ba mu da wani abu a duniya da zai kawo mana salama. Kudi, arziki da sauransu ba za su ba mu Salama ba. Shaye shaye ba zai ba mu salama ba, har ma rubutun sunayenmu a cikin rigistar Ikilisiya ba zai ba mu salama ba.

Hanya daya kadai na samun salama shi ne mu zo wurin Yesu, mu shaida masa zunubanmu mu kuma rabu da su. “In kuwa muka bayyana zunubanmu to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukan rashin adalci.” (1 Yahaya 1:9). Salamar da Yesu yake bayarwa ya fi gaban ganewar mutane (Fibiyawa 4:7). Mutane ba za su iya bayyana wannan salama ba, amma mukan iya jinsu a rayuwarmu idan muka yarda muka bar zunubanmu da abokanmu masu zunubi, muka kuma juyo ga Yesu Kristi da bauta masa. Za mu iya rayu babu salama, amma ba zai yiwu mu tuba ba salama ba, “Ai, mulkin Allah ba ga al’amarin ci da sha yake ba, sai dai ga adalci da salama da farin ciki ta wurin Ruhu Mai Tsarki.” (Romawa 14:17). Idan muka mutu bda salamar Allah a zukatanmu kadai ba, za a marabci ka ga Gidan Salama na Allah ba.

Idan ba mu karbi sarkin Salama a rayuwarmu ba mutuwa zai zo, kuma makomarmu zai zama wuta na jahanama na har abada. Kada ka yarda ka mutu a halin da kake ciki yanzu wannan zai nuna ka hallaka na har abada ke nan. Maganar Allah ta ce mana a Romawa 3:10 cewa, “Babu wani mai adalci babu ko daya.” Hayakin wutar da ke azabtar da su zai ci gaba har abada. Idan kana so ka je sama, akwai abu daya da za ka yi, shi ne ka yi zaman salama da Allah a zuciyarka. “Salamar Almasihu kuma ta mallake zuciyar ka.” (Kolosiyawa 3:15).

A lokacin Krismati, ana tuna mana zuwan Yesu a duniya domin ya kawo salama. A lokacin Easter ana tuna mana yadda aka ki Yesu har aka giciye shi. Kai abokina ko za ka zama daya daga cikin wadanda suka ki shugabanmu ko za ka bude zuciyarka ka karbe shi? Akwai hanya daya kadai na samun salamar Allah a zuciyar ka, shi ne ka durkusa a gabansa, ka shaida masa cewa kai mai zunubi ne, ka roke shi ya zo ya wanke ka ya maida kai nasa. Kome kirkinka, kana bukatar ceto. Kome rashin kirkinka yana shirye ya karbe ka, ba zai kore kowa ba. Idan baka taba samun salamar Allah a rayuwarka ba, sai ka karbe shi yanzu, zaka sami salama mai yawa irin da kalmomi ba za su iya furta ba. (1 Bitrus 1:8).

An yi wani taron bishara a wani wuri, sai wani tsoho ya tashi tsaye yace, "Na yi rayuwa a zamanin sarakuna. A zamanin na farko muka yi ta yaki da juna, da kuma fuskantar wahalu iri iri. A zamani na biyun, an yi yunwa sosai har muka rika cin bera da ciyayi iri iri. A zamanin na ukun abokan gaba suka yi nasara a kanmu har muka zama bayinsu. Amma a wannan zamanin, sai wani sarki ya ziyarce mu. Wannan babban sarki ne, mai kirki, mai son salama, yana da kauna sosai – Yesu shi ne Ubangijinmu daga sama! Ya yi nasara da magabcinmu, ya kuma yi nasara da zukatanmu. Shi ya sa yanzu muna da salama da walwala, kuma muna bege za mu rayu da shi a sama!

Dan'uwa, ka mika kai ga Yesu. A yanzu sai ka bar bin hanyar hallaka, ka juyo ka bi Sarkin Sarakuna da Ubangijin ubangijai. Zai yiwu abokanka da yawa zasu rabu da kai, amma ka tuna Yesu yace "Salamar Almasuhu kuma, ta mallake zuciyarku, domin lalle ga haka aka kira ku in kuna jiki guda." (Kolosiyawa 3:15).

M.R. Gschwend

---

The popular "Heart Book" with its soul-saving message is obtainable in over 500 languages. Many have found salvation even just by looking at the pictures.

Kindly write to us if you are able to assist us with further translations of our free Gospel literature, informing us of the language into which you could translate this Gospel literature. Your assistance would be appreciated.

If you have found salvation in Christ, or have been otherwise blessed through our Gospel literature, please let us know. We would like to thank God with you, and remember you further in our prayers.

For **free** Gospel literature, books and tracts in over 540 languages, write to:

**E-MAIL: info@angp.co.za**

**ALL NATIONS GOSPEL PUBLISHERS**

**P.O. Box 2191, PRETORIA, 0001, R.S.A.**

(A Gospel Literature Mission financed by donations)

(Reg. No. 1961/001798/08)